# ALBASA TA KI HALIN RUWA

NA

KHALID IMAM
LA-3774-97
ENGLISH/HAUSA

SASHIN NAZARIN HARSUNAN NIJERIYA

.WALEJIN ILIMI TA MINNA

AGUSTA, 2000

LANG
4B

# ALBASA TA KI HALIN RUWA

NA
KHALID IMAM
(LA/3774/97)

ENGLISH/HAUSA

SASHIN NAZARIN HARSUNAN
NIJERIYA,

KWALEJIN ILIMI TA MINNA

AGUSTA, 2000.

SERIAL/DOCUMENTATION UNIT
LIBRARY DEPT.
C.O.E. MINNA

# AMINCEWA.

An karanta wannan bincike, an kuma amince da shi, da cewar ya cika ɗaya daga cikin sharuɗɗan samun takardar shaidar N.C.E. a Kwalejin Ilimi ta Jihar Neja da ke Minna.

Sunan mai duba bincike:

AHMAD SAMBO

Rana da kwanan wata:

20/11/2000

Sa hannu:

Sunan Shugabar sashe:

Rana da kwanan wata.

Sa hannu:

# SADAUKARWA.

Na sadaukar da wannan wasan ga mahaifiyata Hajiya Maryam Khalid Saboda tabbatar mini da ta yi cewa ita uwa ce, ma ba da mama. Kamar yadda Hausawa kan ce. Sannan na sadaukar da shi ga mahaifina marigayi Alhaji Khalid Abubakar (Abbani) da kuma kakata marigayiya Hajiya Hauwa Shu'aibu Ɗanjuma (Hajiyar mubi). Allah ya saka musu da alherinsa - Amin.

# GODIYA

Alhamdulillahi masha Allahu Lakuwata illah billahi aliyul azim. Ina fara miƙa godiyata ga Allah subuhanahu wata'ala sarkin da ba shi da abokin tarayya, da ya ba ni ikon gudanar da wannan bincike cikin nasara.

Bayan haka, ina farin cikin miƙa godiya ta musamman ga mahaifina marigayi Alhaji Khalid Abubakar (Abbani) saboda sanya tushen shukar ilimantar da ni da ya yi kafin rasuwarsa. (Allah ya jikansa ya kuma saka masa da Alherinsa). Haka kuma, ba zan manta da miƙa godiyata ta musamman ga mahaifiyata Hajiya Maryam Khalid, saboda tabbatar mini da karin maganar da Hausawa ke yi na cewar, uwa ita ce ma ba da mama. (Na gode, Allah ya saka miki da alherinsa).

Ina kuma farin cikin miƙa godiyata ga Malam Ahmad Sambo (Daraftan Share fagen N.C.E) saboda mahimman shawarwari masu ma'ana da ya ba ni yayin rubuta wannan wasa da kuma gyare-gyare yayin duba wasan. Haka zalika, ina godiya ga Malama Salamatu (Shugabar Sashen Hausa) da Malam Aliyu M. Busa (Young doctor) da Malam Isah A. Fulani na jaridar Tauraruwa da Malam Ibrahim (Sakataren provost C.O.E. Minna) da kuma Hon. Abdulkarim A. Mazakuka (Wakilin Ƙaramar Hukumar Mashegu a majalisar dokoki ta Jihar Neja da ke Minna). Saboda gagarumar gudun mawar da suka ba ni da shawarwari masu alfanu da kuma kuɗi yayin rubata wannan bincike.

Bugu da ƙari, ina godiya ga 'yan uwan mahaifiyata musamman su: Inna Talatu da Inna Asabe da Inna Amina da Kawuna Alhaji U. M. Danjuma da Kakannina marigayiya Hajiya Hauwa (Hajiyar mubi) da Zainab (Abu) sannan kuma ina godiya ga yayata Amina Usman da mijinta Usman Ɗan marka da yayata Umma ta salluwa da kuma yayata Hajiya Kubura da mijinta Alhaji Suleiman A. Mashegu (Deputy Director Federal Ministry of Education, Minna) da yayana Abba khalid da ƙannena su, Muhammad Nuhu (Ɗantani) da Lawan Nuhu da Aishatu Nuhu da mahaifinsu Malam Nuhu Gurmana da Aishatu Khalid (Iyandu) da Abubakar Khalid (Babangida) da Alhaji Hafizu Khalid da kuma, ɗan-autanmu Suleiman Khalid (Abbatiti). Haka kuma, ina godiya ga mijin mahaifiyata Malam Ibrahim Ƙarami Mubi da Binta da matar yayana Hannen Abban rijiya da Abokaina irinsu: Muhuyideen M. Shirawwa da Umar Mohammad Yakasai da Idris Haruna (Naira) da Micheal Ajayi Mai facin tayoyi a garin Bosso da kuma duk sauran waɗan da sunansu bai samu shiga cikin wannan binciken ba, Allah yaka masu da alherinsa-Amin.

# 'YAN WASA

1. **Malam Sodangi-** Malamin makarantar boko ne mai kishin ci-gaban al'ummarsa. Malam sodangi na da mata mai suna Haƙuri da kuma 'ya'ya maza guda biyu , Cinnaka da ƙaninsa Aminu.

2. **Huƙuri-** Uwar gidan Malam Sodangi kuma mahaifiyar Aminu. Mace ce mai haƙuri da son zumunci kuma tana da kishin zuci wajen yin sana'a.

3. **Cinnaka-** Shi ne babban ɗan Malam Sodangi. Cinnaka inuwar giginya ce shi kuma matashi ne mai son kansa sosai, sannan kuma ga ashararanci da neman mata, yana da babban Abokin cin mushe mai suna Yautai.

4. **Malam Ɗanjuma-** Aminin Malam Sodangi ne shi ne kuma mahaifin Bala, Dattijo ne, mai kirki da sanin ya kamata. Hakan nema ya sanya ya auri Haƙuri bayan rasuwar mijinta Malam Sodangi.

5. **Malam Adamu-** Shi ma aminin Malam Sodangi ne kuma mahaifin Zainab. Dattijo ne mai son zumunci da kuma dattako. Malam Adamu makwaɓcin Malam Ɗanjuma ne da kuma Malam Audu.

6. **Malam Audu-** Malam Audu dattijo ne na kwarai kuma Aminin Malam Sodangi ne. Shi ne mahaifin Ɗanladi kuma mijin Inna Talatu.

7. **Aminu-** Ɗa ne wajen Malam Sodangi da Haƙuri, Aminu yaro ne mai ƙoƙari a makaranta. Shima kamar mahaifinsa akwai shi da kishin ci-gaban al'ummarsa don haka da ya sami kuɗi ya bude makarantu da kamfanoni a garinsu. Aminu mutun ne mai kyauta sosai.

8. **Kande-** Ƙanwar Malam Sodangi ce kuma ita ce wadda ta ci-gaba da kulawa da Aminu bayan Haƙuri ta yi aure.

9. **Ɗanladi -** Ɗan Malam Audu ne kuma abokin Aminu.

10. **Bala-** Ɗan Malam Ɗanjuma ne shi kuma saurayin Zainab da ta gujewa.

11. **Ɗantani -** Abokinsu Cinnaka da Yautai ne, amma shi halinsa ya shabambam da na su, don haka ba su fiya shan inuwa guda tare ba don son gaskiyarsa.

12. **Yaron Malam-** Almajiri ne kuma abokinsu Aminu, shi matashine mai hangen nesa da kyamar zalunci. Sannan kuma yana da sha'awar haɗa ilimin boko da na allo ko islamiyya.

13. **Zainab-** Yarinya ce kyakyawa ɗiyar Malam Adamu. Ita ce buduwar Bala da ta gujeshi ta komawa Cinnaka don kwaɗayin abin hannunsa, a ƙarshe Cinnaka ya sanya ta tayi biyu babu sakamakon korar karen da ya yi mata bayan ya gama cin moriyar ganga.

14. **Asabe-** Matar Malam Adamu ce kuma mahaifiyar Zainab kuma aminiyar Haƙuri.

15. **Inna Talatu-** Matar Malam Audu ce kuma mahaifiyar Danladi, ɗattijowace mai son yara su sa ido a karatu. Sannan ga ta da kirki da zumunci.

16. **Yautai-** Babban abokin cin mushen Cinnaka ne shi, matashi ne mara kirki ga kuma haɗa fitina. Yautai ba ya taimakon kowa in ban da mata ƙabilu soboda wai sun fi daɗin harka a cewarsa. Kamar Cinnaka abokinsa shima mashayi ne kuma ga shi dangin shirwa. Yautai yana wulakanta al'adun iyayensa da kakanni ga kuma girmama na Turawa.

17. **Tanko-** Abokin Cinnaka ne da Yautai.

# GABATAR WA.

Wannan wasa hannunka mai sanda ne kuma an shirya shi ne kan wani marayan yaro mai ƙoƙarin gaske a makaranta da kuma kishin zuci. Sunan wannan yaro Aminu. Mahaifinsa ya rasu ya bar shi tare da mahaifiyarsa mai suna Haƙuri da kuma wansa mai suna Cinnaka. Kamar yawancin yaddan'yan boko ke yi Cinnaka ya yi biris da rayiwar matar mahaifinsa da kuma ta ɗan-uwansa ya zama inuwar giginya..... Ban da sharholiya da almubazzaranci da Ashararanci babu abin da Cinnaka da abokin cin mushensa mai suna Yautai suke yi. Hakan kuwa ya faru ne saboda watsin da suka yi da tarbiyar da suka ginu akai wadda mahaifin Cinnaka Malam Sodangi da sauran dattawa 'yan-uwansa suka gina su akanta ta taimakon juna da kaunar juna.

Da yake albasa ba ta yi halin ruwa ba, Cinnaka da Yautai sai suka rungumi ɗabi'un Turawa maimakon nasu da suka gada daga iyaye da kakanni. Hausawa dai na cewa, "Babu maraya sai rago". Sanin wannan ya ba Aminu da mahaifiyarsa Haƙuri ƙarfin gyiwar zage dantse wajen yin sana'a domin zomo ba ya kamuwa daga zaune. Da ya-ke Cinnaka samu ka ƙi dangi ne, ko da Aminu ya kammala karatunsa sai Yayansa Cinnaka ya ƙi tallafa masa ya sami aiki duk da cewar yana bawa wasu. Amma da ya ke hanyar Allah tafi ta Cali yawa, sai Aminu ya sami aiki da ƙyar bayan ya share shekaru yana nema.

Cinnaka da Yautai zasu tsiyace, su koma ba su ga tsuntsu ba su ga tarko. Amma da yake hannun mutum ba ya ruɓewa ya yanke ya yar sai Aminu ya rungumi Cinnaka tankar wanda bai ta ɓa ɓata masa ba. Amma kashi! Hali zanan dutse kuma shi wanda ya yi nisa ba ya jin kira. Domin haka sai hassada da in giza mai kantu ruwan da Yautai ya kewa Cinnaka ya hana shi farfaɗowa. Ai da ma idan farauta ta ƙi mutum kunkuruma sai ya tsare masa. Aƙoƙarin Cinnaka da Yautai na su halaka Aminu sai reshe ya juye da mujiya. Don haka marigayi Dafta Mamman Shata ke cewa, "mu gargaɗi mai gina ramin mugunta....".

Aminu ko da yake zuciyarsa ta alheri ce a kullum likkafa sai ƙara ci-gaba take yi. Don haka, sai suka haɗa hannu shi da Ɗantani suka rika giggina makarantun boko da na Islamiyya a garinsu wannan ya sanya yara suka riƙa makarantu. Kamfanonin kuwa da Aminu ya kakkafa a garinsu, sun sanya garin ya bunƙasa, mutane suka sami aikin yi, rayuwa ta saukaka ga talakawa.

***Khalid Imam.***

(Agusta 2000)

# ABUBUWAN DA KE CIKI

Amincewa........................................................................................................ii
Sadaukarwa ....................................................................................................iii
Godiya ............................................................................................................iv
'Yan-wasa .......................................................................................................v-vii
Gabatarwa .......................................................................................................viii
Shiga ta daya...................................................................................................1-7
Shiga ta biyu ...................................................................................................7-13.
Shiga ta uku ....................................................................................................13-21
Shiga ta hudu ..................................................................................................21-26
Shiga ta biyar ..................................................................................................26-35
Ƙarshe ............................................................................................................35.

# KASHI NA ƊAYA

**FITOWA TA ƊAYA:** A ƘOFAR GIDAN MALAM ƊANJUMA.

*Bis ta ɗauri sin, (Niyyar tashi) Bari ka gani in shiga gida in fito mana da abinci tun kafin su Malam Audu su iso. Washi! Jikin tsufa. (Ya ji sallama) Alaikkas salam.*

**Malam Audu:** *(Shiga)* Ƙar dai gyangyaɗi kake?

**Malam Ɗanjuma:** *(Ya amsa)* ko kaɗan! *(Cikin fara'a)* lale! Har ka ƙara so? *(Gaisuwa)* yanzu na ke cewa bari na shiga gida na fito mana da.......

**Malam Audu:** *(Ya katse masa hanzari)* Malam Adamu bai ƙaraso ba ashe! Ai ko tare muka yi sallar isha'i. *(Jinkiri)* Af! Ai ga shi nan tafe.

**Malam Ɗanjuma:** *(Cikin fara'a)* Ɗan halas ka ki ambato!

**Malam Adamu:** *(Shiga)* salamu alaikum, Malam Audu ashe har ka iso? *(Ya ajiye abincin da ke hannusa).*

**Baki Ɗaya:** Wa'alaikumussalamu. *(Gaisuwa)*

**Malam Audu:** Malam Ɗanjuma ai sai ka shiga ka fito da abincin ko? Af! Kar na manta Malam Sodangi fa..............

**Malam Adamu:** *(Ya katse masa hanzari)* Ai sai kayi zamanka Malam Ɗanjuma don mu fara cin wannan abincin tunda ga Bala nan tafe ya ɗauko! *(Jimkiri)* Malam Audu kana maganar Malam Sodangi kar dai in ce ya sake komawa birnin tarayya daga dawowarsa jiya-jiya.

**Bala:** *(Shiga)* salamu alaikum. *(Ya durkusa cikin ladabi da nutsuwa, ya gaishe su)* Bari in ɗauko abincin, ko an fito da shi ne?



SERIAL/DOCUMENTATION UNIT
LIBRARY DEPT.
C.O.E. MINNA

**Malam Audu**: A'a, maza shiga ka fito mana da shi ko mayi sauri mu je gidan Malam Sodangi dubiya. *(Bala na shiga gida)* Ince ko dai an taso daga makarantar, ba gudowa ka yi ba?

**Bala** *(Ya amsa)* Eh! An taso Baba. *(Ya shiga gida)*

**Malam Adamu**: Ai sai mu fara cin abincin ko!

**Malam Audu**: *(Cikin ba'a)* Yau dai tun da na riga ka zuwa nawa abincin zamu fara ci ko yaya ka gani Malam Ɗanjuma?

**Malam Adamu**: *(Cikin raha)* A'a, Malam Audu, kuma abin yau har da zolaya? To! Shi ke nan sai mu fara da nasa din.

**Malam Ɗanjuma**: Ina ruwan basabamba. *(Ya matso da akushin Malam Audu tsakiyarsu, sannan ya buɗa)* Lallai! Bari na gyara zama tun da naga abin nayi ne.

**Malam Adamu**: *(Cikin mamaki)* Malam Ɗanjuma, ashe kaima ɗan-uwana ne ba ka wasa da ɗan-wake? Lallai! Kakarmu ta yanke saka ke nan yau. *(Bala ya shigo rike da kwanukan abinci.)* Yauwa Bala! Miko mini ruwan nan.

**Bala:** To! Baba ga shi. *(Ya durkusa cinkin nutsuwa, ya ba shi ruwan, sannan ya shiga gida).*

**Malam Audu**: *(Ya dubi Bala na shiga gida)* oh! Malam Adamu don Allah dubi yadda Bala ya fara zama saurayi. Ashe gaskiyar Malam Sodangi da ya dage kan sai mun sanya su makarantar boko da wuri.

**Malam Adamu**: Kai dai dube shi kamar ba shi aka haifa ba shekararda Ya'u marini ya je gabas sauke farali. *(Ya kai ɗan-wake baki)* Oh! Akwana a tashi dai ba wuya! Malam Audu ai ko yanzo aka bawa Bala mata riƙewa zai yi tsaf, ko ba haka ba?

**Malam Audu**: Ƙwarai! *(Jinkiri)* kai da kake wannan batu Malam Adamu in ban da bokon da yake yi ai muna kamar shekarunsa iyayenmu su ka yi mana auren fari. *(Ya jawo kwanon abincin Malam Audu)* Allah dai ya sakawa Malam Sodangi domin ilimin zamani da ya sanya 'ya'yanmu ashe ba ƙaramin jari ba ne!

**Malam Ɗanjuma**: Sosai! Maganarka duste Malam Audu. domin naga amfaninsa jiya.

**Malam Audu**: *(Yana zubawa burabuskon gidan Malam Adamu miyar tashe).* Malam Ɗanjuma kace, "jiya ka ga amfaninsa." To, kamar yaya?

**Malam Ɗanjuma**: *(Bayan ya kai burabusko baki)* Hmm! Ai jiya da na sami wasiƙa daga ɗan-uwana da ke Bosso shi Balan ne ya karanta mini. *(Jinkiri)* kun san da Malam Sodangi ke karanta mini.

**Malam Adamu**: Ai dadin ilimin ke nan, kuma shi ilimi daman amfaninsa bai wuce aiki da shi ba!

**Malam Audu**: *(Ya sha ruwa)* Ai wato Malam Ɗanjuma ina ganin wautar 'ya'yan yau da suke auren ƙabilun da ba su iya girka musu irin abincinmu na gargajiya ba, sai dai shinkafa ko shayi.

**Malam Ɗanjuma**: *(Cikin barkwanci)* Musamman ma dai burabusko da taushe!

**Malam Audu**: Wallahi ba fa santi na ke ba! *(Suka bushe da dariya)* ku naga wasa kuke mayar da maganar tawa. *(Jinkiri)* kai! Allah wadaran naka ya lalace. To, in ba lalacewa da kuma cigaban mai hakan rijiya ba, yaushe 'ya'yanmu zasu dinga auren kara da kiyashi........

**Malam Ɗanjuma**: Haba! Malam Audu kar dai ka yi tuya kamance albasa. Ni ina ganin laifin na gun namu 'ya'yan mata.

**Malam Adamu**: Kamar yaya fa?

**Malam Ɗanjuma**: *(Ya yi tsaki)* Tsm! Yaran da son jiki da kuma ƙaryar boko duk sun sangartar da su. Don abin takaici haka suke tafiya gidajen mazajensu suna kwaɓa abinci su da ƙabilun babu bambamci. *(Jinkiri)* Allah dai ya sauwake. *(Ya kama wanke hannu)* Ai dolenmu iyaye mu tashi tsaye domin muma wasunmu sakaci gare su. *(Ya dubi almajirin da ke gefe)*. Bismillah Yaron Malam, ai mun hattama.

**Yaron Malam:** Allah ya biya niyya, ya kuma biya bukata. *(Ya juye sauran abincin a ƙoƙon bararsa)* Allah saka da Alheri.

**Malam Ɗanjuma**: Amin suma amin. *(Bala ya shiga)* Ina zaka? Zo miƙa kayan abincin nan. *(Ya dubi aminansa)* Ai sai mu yi niyyar dubiyar da ke gabanmu Ko?

**Malam Audu:** *(Ya dubi Bala)* Bala in ka kai akushin ka cewa, Innar taka mun tafi duba Malam Sodangi don haka idan an zo nema-na a jira ni ba daɗewa zamu yi ba.

**Bala:** To! A dawo lafiya. Sai kun dawo. *(Ya dauki kayan abinci ya nufi kaiwa)*. Allah ya kiyaye hanya.

**Baki Ɗaya** Amin! *(Sun nufi gidan Malam Sodangi)* Bismillanmu. *(Suka cigaba da hirar-su suna tafiya)* Fita.

**FITOWA TA BIYU:** A ƘOFAR GIDAN MALAM ADAMU.

*Mun dai ga Bala ya nufi gidan Malam Adamu da kuma Malam Audu riƙi - riƙi da kaya. Gashi can dai ya isa ƙofar gidan Malam Adamu kuma ya hangi Zainab ɗiyarsa tana dawowa daga aike riƙe da leda a hannu zata shiga gida. Bari mu ji yadda za su tattauna. Ku biyo ni don jin irin wainar da za a toya tsakaninsu.*

**Bala**: *(Shiga)* shi ke nan faɗuwa tazo dai-dai da zama, ga Zainab nan tafe. Ina ma a ce gida za ta shiga? *(Yana magana shi kaɗai)* Zainab, Zainab *(ya sake ɗaga murya)* Zainab ba kya ji ina ta kiranki? Sauri kike yi haka? Haba! Amma ai mun gaisa duk saurin da kike yi. *(Ya yi murmushi)* Oh! Zainab manya.

**Zainab**: *(Ta waiwayo)* Au! Bala ashe kai ne kake ƙwalan kira daman? Don Allah ka yi haƙuri, na ɗauka irin samarin nan ne masu kiranye-kiranyen 'yan matan tsiya.( *Gaisuwa)* Bala ashe Talaka na ganinka *(Cikin murmushi)* Amma fa gaskiya ka ɓuya.

**Bala:** *(Ya gyara murya)* Daman ai haka zaki ce mana. Amma ni da ke wa ya ɓuya? Don Allah in gida Zaki shiga taimakamin da waɗannan..... *(Ya miƙa mata kwanukan hannunsa)* Amma ina fatan ban sa ki aiki ba?

**Zainab**: *(Cikin murmushi)* Amma kaima dai Bala sai a barka, don ka sanya ni wannan ɗan aikin ai ba wani abu. *(Jinkiri)* Ai da kai da kaya duk mallakar wuya ne. *(Kunya ta kamata)* Zan shiga gida. *(Kanta a sunkuye)*.

**Bala:** Haba! Zainab har zaki shiga gida ke nan. To! Na gode, sai kin gannin gobe nazo miki hira.

**Zainab**: Hmm! Don Allah rabani da alƙawarin 'yan nefu. Ai kai daman Bala na sanka wajen ƙin cika alƙawari, To! Karya alƙawari dai ka san ma'aiki na cewa, "Na ɗaya daga cikin alamun munafukai".

**Bala:** *(Ya noƙar da kai, alamar rashin gaskiya)* Haba! Wannan karon ba wasa, tun da nace miki zanzo babu wasa insha Allah. Ko rannanma aiyuka ne su ka yi mini yawa. Don Allah ki yi haƙari. Zan zo insha Allahu.

**Zainab**: *(Cikin ba'a)* To, Allah ya sa in har da gaske kake yi. *(Ta fara tafiya)* Bari na shiga gida don yakumbo ce ta aike ni.

**Bala:** To, Malama zainabu abu mai tagwayen suna ya banga kin yi murmushi ba balle nasan ko kin yafe mini laifin nawa. *(Ta yi murmushi)* Ko ke fa! Sai da safe ke nan, ki fa sa idon zuwa na goben!

**Zainab**: To, sai kazo. *(Jinkiri)* Allah kuma ya kai mu goben da rai da lafiya *(Ta shiga gida)*



SERIAL/DOCUMENTATION UNIT
LIBRARY DEPT.
C.O.E. MINNA

**Bala:** Amin. *(Ya fita, ya nufi gidan Malam Audu.)*

**FITOWA TA UKU:** A GIDAN MALAM AUDU:

*Inna Talatu matar Malam Audu na zaune kan tabarmar karauni a ƙofar ɗakinta tana lazimi. Shi ko Bala da shigowarsa sai ya zarce gun wanke-wanke ya ajiye akushin da ya kawo. Sannan ya ƙarasa gun ta don ya gaisheta. Ku biyo ni don jin yadda za su ƙare.*

**Bala:** *(Shiga)* Salamu alaikum.*(Gaisuwa)* ga akushi nan in ji Baba

**Inna Talatu:** *(Ta amsa)* To! Yaya Gyatumartaka? Ince ko dai tana tafiya. *(Ta Lura kansa babu Hula)*. A'aha! Bala yaya kuma ana yabonka sallah kana neman kasa alwala. *(Cikin faɗa-faɗa)* Ina kuma ka bar tagiyartaka? Don Allah ka daina barin kanka sheɗan na yi maka fitsari. (*Jinkiri*) Ai cikakkiyar sutura ita ce mutum domin duk inda ya shiga amfi ɗaukansa da mutunci.

**Bala:** *(Kansa a sunkuye)*To, Inna. *(Jinkiri)* In Allah ya so ban ƙara fitowa babu hula bisa kai na!

**Inna Talatu:** *(Cikin farin cikin)* Yauwa! Allah ya yi maka albarka ka dai dinga sa ido da kuma jin abubuwan da iyaye ke fada maka don wataran zaka ga alfanunsu, ka ji ko?

**Bala:** To! Inna na gode, ni zan ƙarasa gida. *(Ya miƙe daga inda ya durƙusa)* sai da safe.

**Inna Talatu:** Ga goro ka kaiwa Gyatumartaka. *(Ta miƙa masa)* ka ce ina gaisheta, ka ji ko? Mu kwana lafiya.*(Har ya kai zaure, sai ta ƙwala masa kira)* Balá, Bala zo in ba ka saƙo mana.

**Bala:** *(Ya dawo da sauri)* To, Inna, ga ni.

**Inna Talatu:** Don Allah in ka je gida, ka faɗa mata cewa gobe zan zo ta raka ni barkar 'yar aminiyata Maryam da ta haihu shekaran jiya. Kar fa ka manta. *(Ya amsa)* sai da safe, Allah ya tashe mu lafiya.

**Bala:** Amin suma amin *(Ya nufi ƙofa)* sai gobe. *(Fita)*

**FITOWA TA HUƊU:** A GIDAN MALAM SODANGI.

*To, jama'a Hausawa dai na cewa, "idan ajali yayi kira ko ba ciwo aje". Idan ba mu manta ba Malam Audu da aminansa mun bar su sun nufi gidan Malam Sodangi don duba yadda ya ƙara ji da jiki, ku biyo ni don jin abin da ya afku a gidan.*

**Malam Audu:** *(Shiga)* Subhanallahi, lafiya kake kuka? *(Aminu ya cigaba da kuka bai amsa ba)* Malam Adamu ni fa na tsorata, kar dai jikin mahaifin nasa ne ya yi tsanani.

**Malam Ɗanjuma:** Innalillahi wa ina ilaihir raji'una, Malam Audu ai tun da ya kasa buɗa baki ya yi mana bayani sai mu sallama, mu shiga ciki.*(su ka shiga suna mamakin kukan Aminu)*

**Malam Adamu:** *(Matar Malam Sodangi na kuka)* Allahu akbar, Inna lillahi wa ina ilaihir raji'una, *(Gumi ya karyo masa)*Haƙuri ai sai ki yi haƙuri ki bar kukan haka. *(Ya dubi Malam Audu)* Don Allah Malam Audu maza ruga ka shaidawa liman da sauran jama'a cewar........

**Malam Audu:** *(Ya miƙe)* Allah mai girma. *(Hawaye na zuba daga idanunsa)* Allah Akbar, Allah mai yi yadda ya so. *(Ya fita yana ta salati)*

**Malam Ɗanjuma:** *(Ya dubi Haƙuri)* Ai ba kuka za ki yi masa ba Haƙuri, addu'a za ki yi masa ta Allah ya yi masa rahama.*(Ta shiga ɗakinta, tana share hawayen idanunta)* Allahu Akbar Kabiram. Allah ya jikanmu, ya jikan Malam Sodangi

*Bayan Liman da sauran jama'a sun taru, sai suka yanke shawara cewa, tun da dare bai yi sosai ba,sai a yi jana'izar Malam Sodangi domin a yi masa sutura. Hakan kuwa aka yi. Allah ya jikanmu baki ɗaya idan lokacinmu ya yi. Amin suma amin.*

## SHIGA TA BIYU

**FITOWA TA ƊAYA:** GIDAN MARIGAYI MALAM SODANGI.

*Allahu Akbar, Allah mai yi yadda ya so. Tun da Malam Sodangi ya koma ga Rabbil-izzati. Rayiwa a gidansa sai ta canza zane. Kaico!Da ma ita duniya rawar 'yan mata ce... Bari dai in miƙa ku gidan don jin yadda rayiwa ta rikice wa Haƙuri da Aminu ɗanta. Ku biyo ni.*

**Haƙuri:** *(Shiga)* Aminu, Aminu ko barci ka kwanta ne? *(Ta sake ɗaga murya)* Aminu! *(Ya amsa)* Haba! Kuma daga cin abinci sai ka yi shiru a ɗaki kamar an aiki bawa garinsu.

**Aminu:** *(Ya fito, ya durkusa)* Gani! Dama na gama cin abincin, Zan fito kenan sai ki ka kira ni.

**Haƙuri:** *(Cikin faɗa)* Haba! Sai ka ce mara kunne, ace duk irin kwalla maka kiran nan da na yi..... *(Ta kwantar da murya)* Ai sai ka yi harama ka zo ka tafi tallan gurasar da ke gabanka.

**Aminu:** *(Ya amsa cikin ladabi)* To! Ta nawa ki ka ƙirga, ko yau ma gurasar kamar ta jiya ce ? *(Ya ɗau farantin gurasar ya ɗora a ka)*

**Haƙuri:** Eh! Kamar ta jiya na ƙirga maka. Maza ka mai da kai ka sayar da wuri kafin lokacin makarantar muhammadiya ya yi ka dawo, ka ji ko? Allah ya bada sa'a.

**Aminu:** *(Ya amsa)* Amin . *(Ya nufi ƙofa)* Na tafi, sai na dawo.

**Haƙuri:** Allah ya ki yaye, ya kuma ba da da kasuwa. *(jinkiri)* Don Allah kar ka tsaya wasa, ka ji ko?

**Aminu:** *(Ya amsa)* To! sai na dawo. *(Ya fiṭa, yana talla)* Ga gurasa da dumi, a sai gurasa..................

**FITOWA TA BIYU:** A DANDALIN SAMARI

*To, mun dai ga Aminu ya tafi talla. Ga shi can ya nufi dandali yana talla. Ku biyo ni don jin wainar da za a taya.*

**Ɗantani:** *( Shiga)* Assalamu alikum. *(Ya miƙawa Yautai hannu da ke zaune kan benci suna hira da Tanko)* Yautai, a she ana ganinka. *(Gaisuwa)* Wancan Yaron kamar gurasa na ji ya na talla ko?

**Yautai:** *(Ya yi dariya)* Ƙwarai kuwa! Kar dai in ce tsimagiyar kan hanya ke damunka?

**Ɗantani:** Kamar ka shiga zuciyata. *(jinkiri)* Kai yaro mai gurasa kawo nan. *(Aminu ya na nufo so)* Af! Ashe ma Aminu ƙanin Cinnaka ne!

**Yautai:** Au! Kai da baka gane shi ba.*(Aminu ya iso gun su)*. Aminu nawa-nawa ce gurasar taka?

**Aminu:** *(Bayan ya gaishesu)* Ai saura ta ₦20 kawai.

**Tanko:** To! Ba mu ta duka *(Ya sanya hannu a aljihu)* Yautai ko dai ta yi mana kadan ne? Aminu amshi kuɗin nan karɓo mana zoɓo gun yarinyar can. *(Aminu ya karɓi kuɗin, ya ruga, ya sayo)*. Yauwa Aminu, to, karɓi kuɗin ka kaima.

**Aminu:** *(Ya karɓa)* To, sai an jiman ku.*(Ya fita, ya nufi gida)*

**Ɗantani:** *(Yana cikin cin gurasa da zoɓo, sai ya lura Yautai ya ƙi ci)* A' a, Yautai ya naga kana kallonmu. Ko dai ka ƙoshi ne?

**Yautai:** *(Ya yi dariya)* Amma dai kai ma Ɗantani da wasa ka ke yi. *(ya girgiza kai, ya na mamaki)* Haba! Ai ni tuni na bar cin irin waɗannan yamen-yamen tsiyar da dai mitfay ne ko kek da sai na taya ku ci, amma in har yanzu ina cin irinsu, ai kenan babu bambamci tsakanina da su Tanko wadanda iyakar bokonsu firamare.

**Tanko:** *(Ya yi tsaki)* Tsm ! Yautai manya, to ina ruwan boko da abinci. Ka ce kai da Abokinka Cinnaka Ɗanjuma ne da Ɗanjummai.

**Yantai:** Oh! Kai sai yau ka sani. *(Cikin murmushi)* Ai ba za mu fita karatu har ƙasar Amurika ba, idanmu ya buɗe, sannan mu dawo muna rayiwa irin ta makafi.

**Ɗantani:** Kaico! Da dai ba mu san asalin ungulu ba sai tace daga misira take. Haba! Yautai kar fa kamanta kowa ya bar gida, gida ta bar shi. *(Yautai ya miƙe zai tafi)* Au, ba dai tafiya za ka yi ba?

**Yautai:** *(Ya amsa)* Kwarai! Tun da hirar ta koma habaici, ai ina ga gwara in isa gida na yi abin da zai fisshe ni,*(Ya kama tafiya)* kunga tafiya ta *(Ya fita)*.

**Tanko:** Umma ta gai da Aisha. *(Ya dubi Ɗantani)* Iallail *(Cikin fushi)*



SERIAL/DOCUMENTATION UNIT
LIBRARY DEPT.
C.O.E. MINNA

Hausawa sun yi gaskiya da su ke cewa, "Daga kin gaskiya sai bata". *(jinkiri)* kai, Allah raba mu da irin wannan cigaban mai haƙan rijiya irin na su Yautai!

**Ɗantani:** *(Ya amsa)* Amin. *(Ya yi dariya.)* Ka san Hausawa sun yi gaskiya da suke cewa, "Gwano ba ya jin warin jikinsa,". Kuma, "wai shi laifi tudu ne, sai mutum ya take nasa ya hango na wani". *(Ya miƙe shi ma zai tafi)* Allah dai ya sa su gane, sannan kuma ya kare mu daga cigaban mai hakan rijiya irin nasu Yautai da Cinnaka.

**Tanko:**
**~~Dantani:~~** *(Ya katse masa hanzari)* Haba ! Allah ya tsari gatari da saran shuka. (suka yi salama, *suka fita ta hanya dabam dabam).*

**FITOWA TA UKU :** A GIDAN KANDE MAI KITSO.

*A cikin tsakar gidan kande mai kitso, Hakuri na zaune Kanwar tsohon mijinta marigayi Malam Sodangi na yi mata kitso. Bari mu ji hirar da suke yi. Ku biyo ni*

**Haƙuri:** *(Shiga)* wai! Matar gidan nan yau na da niyyar yi mini kitson nan kuwa?

**Kande:** Ni Kande na isa naƙi yi wa uwar gidana kitso! Kibiyar kitson ce na ke nema tuni.*(jinkiri)* Haba! don Allah kwantar da hankalinki tamkar tsumma a ruwa, domin gani nan zuwa yanzun nan.

**Haƙuri:** Ai naga kin shige ɗaka kin yi shiru kamar an aiki bawa garinsu ne.

**Kande:** *(Ta-sa kibiya ta tsaga gashin, sannan ta fara Kitson)* Af ! Ai gwara da na tuna. Amma a gaskiya Haƙuri kirkinki yawa gareshi.

**Haƙuri:** Ko ? Ai haka daman nasan zaki ce. To, wani laifin kuma za ki ce na yi!

**Kande:** Ai kinfi kowa sani! *(Ta cigaba da kitso bayan ta shafa mai a tsagar da ta yi)* Yanzu, a ce Ɗan nawa na ciki na halas - malak ya sami lambar yabo a makaranta ta ɗalibin da yafi kowa kwazo amma sai dai na ji labari a gari.

**Hakuri:** Don Allah ki yi hakuri, kin san yau-yau da safen nan kafin na taho nan nima ya zo mini da labarin, kuma daman ina da niyyar na fada miki yanzu kafin na turu shi da kanshi ya nuna miki takaddar da kuma kyautar da aka bashi in na koma gida.

**Kande:** To, shi ke nan. Ai da har na yi fushi. *(Cikin muma)* shin gaske ne cewa, an tura shi makarantar kwalejin kwana?

**Hakuri:** Eh! *(Ta amsa)* Oh! Amma dai zancen duniya baya buya. Wa yazo ya gaya miki wannan labarin ko dai dan naki nan ya fara biyawa ne kafin ya isa gida?

**Kande:** Ko kadan, Malam Audu ne ya fada mini dazun nan suka bar nan shi da mutumin naki malam ...... *(Ta zolayeta)* Haba! ban sunan sa mana sabon Yayan nawa.

**Hakuri:** Ke dai Kande ba kya rabo da zolaya.

**Kande:** Zolaya ko gaskiya. *(Ta gama kitso)* Ai ni abin farin ciki ne a gare ni idan Allah ya tabbatar da aurenki da Malam Danjuma. *(Ta-na murmushi)* Domin tun da uwar gidansa ta rasu ya koma gwauron karfi da yaji.

**Hakuri:** Kin ga ni zan tafi gida, don ke surutunki ba karewa yake yi ba. *(Ta mike tsaye.)* Ga goro kin tauna. *(Ta mika mata)* sai na ganki. *(Kande ta karbi goron, sannan ta rakata har zuwa kofar zaure)* In mai gidan naki ya dawo kin ce masa ina gaishe shi, sai an jima. *(Ta fita zuwa gida, ita kuma Kande ta koma cikin gida).*

**FITOWA TA HUDU:** A KAN HANYA

*Malam Audu da makwabcinsa Malam Adamu sun gamu a hanya. Bari in hada ku da su, don jin abin da suke tattaunawa.*

**Malam Audu:** *(Shiga)* A'a, kamar Malam Adamu ke tafe, ko dai idan nawa gizon tsofa ya cinye shi ne? Af, ai ko shi ne!.

**Malam Adamu:** Salamu Alaikum *(Ya mika masa hannu)* In ce ko dai lafiya na ganka cikin sauri? (Gaisuwa)

**Malam Audu**: Lafiyar ke nan, ai dama gidanka zani.

**Malam Adamu**: Ai shi ke nan faɗuwa tazo daidai da zama.*(jinkiri)*. To, ai sai mu ƙarasa gidan ko?

**Malam Audu**: A'a, ai ko nan ma sai mu gana domin dama ina son na ƙarasa gidan Alhaji Musa ne domin yi masa murnar zaben da ɗansa ya yi nasara na 'yan majalisar tarayya.

**Malam Adamu**: To, ai shi ke nan, kai na ke sauraro!

**Malam Audu**: Daman ina son in ganka ne don mu shawarta kan irin taimakon da ya dace mu yi kan maganar makarantar Aminun Malam Sodangi. Ka san yau satinsa kusan guda a gida, tun da aka koro shi daga makaranta kan biyan kuɗin jarrabawa.

**Malam Adamu**: Lallai! Malam Audu kazo da hanzari. Kuma dama ni kaina naso yau idan mun haɗu gun cin abinci na tada maganar. *(Jinkiri)* Tunda 'ya'yansa Cinnaka arzikinsa ya zama na ashararanci. Kuma mun fahimci bashi da niyyar taimakawa Aminun wajen biya masa kuɗin yin jarrabawar, mu ba ma sa ido ba, ko ba haka ba?

**Malam Audu**: Ƙwarai! Yanzu dai abinda na ga yafi da cewa shi ne mu haɗa kuɗin mu ba shi ya kai, ya biya, domin ya koma, ya rubuta jarrabawarsa.

**Malam Adamu**: Wannan kam dai-dai ne! Kaga an jima in mun haɗu gun cin abinci sai mu sannar da Malam Ɗanjuma. *(Suka haɗa kuɗin, Malam Audu ya ajiye gunsa)* To, Malam Audu bari na ƙarasa gida, sai ka dawo daga gidan Alhajin. *(Suka yi sallama, suka fita ta hanya daban-daban).*

**FITOWA TA BIYAR**: A ƘOFAR GIDAN MALAM ƊANJUMA

*"Alheri danko ne ba ya faɗuwa ƙasa banza". Kamar yadda masu iya magana suke cewa. Don haka ake son mutum ya dinga shuka alheri a koyaushe cikin rayuwarsa domin Allah kawai ya bar wa kansa sanin lokacin da zai girbe abin da ya shuka. Idan ku na biye da ni mun bar Malam Audu da Malam Adamu sun haɗa kuɗin biyawa Aminu kuɗin jarrrabawa. To, ga su can sun kammala cin abinci kamar yadda suka saba. Bari muji hirar da suke yi. Ku biyo ni.*

**Malam Adamu**: Gaskiyarka Malam Audu. Af! Malam Audu, ka ko yiwa Malam Ɗanjuma bayanin maganar da muka yi ɗazu. (Malam Audu ya yi masa bayani dalla-dalla) To, yanzu yaya za mu yi ke nan.

**Malam Ɗanjuma**: Wallahi na ji daɗin wannan abu da kuka yi, kuma ni babu abinda zance illah Allah ya saka muku da Alherinsa, ya kuma bar zumunci. Don haka nima ga nawa. *(Ya miƙawa Malam Audu)* ku haɗa in ya so sai ku aika a kaiwa Yakumbonsa Kande mai kitso don ta kira shi ta ba shi. *(Jinkiri)* Ni kuma idan na shiga gida zan shaidawa mahaifiyartasa yadda ku ka yi.

**Malam Audu**: To, shi ke nan zan isa gida, sai da safe ke nan domin jikin nawa ne ba na jin daɗinsa sosai.

**Malam Adamu**: Allah ya sauwaƙe! Amma dai Malam Audu da ka daure mun ƙarasa gidan Kanden mun bata waɗannan kuɗin tare da na so hakan. Kasan Mallam Ɗanjuma ba zuwa zamu yi da shi ba.

**Malam Audu** To, ai sai mu isa babu komai, *(Su-ka yi sallama da Malam Ɗanjuma)*, suka nufi gidan Kande, *(shi kuma ya shiga gida)*. Fita.

### SHIGA TA UKU

**FITOWA TA FARKO**: A OFISHIN CINNAKA

*Cinnaka dai likkafa sai kara ci-gaba ta ke yi, domin bai cika shekara uku da dawowa daga ƙasar Amurika ba, sai ya sake samun damar ƙaro karatu a ƙasar Ingila. Ya na dawowa daga kwas ɗin, sai aka ba shi muƙamin babban daraftan kuɗi a ma'aikatar sifuri. Kash! Amma maimakon ya rungumi tarbiyar da magabatansa suka gina shi a kai, ta tallafawa al'ummarsa don ta bunkasa, sai shi da abokin cin mushensa Yautai suka zama dangin shirwa da kuma samu aki dangi. Hausawa dai sun yi gaskiya da suke cewa, "Garin banza a farau-faran woƒi yake ƙarewa." Ga dai Cinnaka can da abokinsa Yautai, don jin yadda suke kashe makudan kuɗaɗen da suke samu ta hanyar yin sama da faɗi a ofishinsu. Ku biyo ni.*

**Cinnaka**: *(Yana a jiye kan tarho, sai ya ji ana kwankwasa ƙofar ofishinsa)* Yas! *(Yana kallon ƙafa)* Aha! Lallai ɗan halas ka ki ambato. *(Ya miƙa masa hannu)* Bismillah! Ai yanzun nan na gama tambayarka a waya.

**Yautai**: *(Ya zauna kan kujera)* Ai na ɗauka ka fita birek da har zan fasa zuwa in duba ko kana ofis.

**Cinnaka**: Ai ni yanzu a ofishina nake cin birek domin cuwa-cuwa na ci sosai 'yan kwanakin nan. Don haka ban son motsawa nesa don kar banza ta zo ta wuce ni.

**Yautai**: *(Suka tafa)* Haka nake son ji mutumina.*(Dariyar mugunta, haɗe da kirari)*. Cinnaka kake baka san na gida ba. *(Su ka sake tafa hannu)* Af! yaya banga mutumiyarka ba da zan shigo, ko tana hutu ne?

**Cinnaka:** Don Allah kar ka ɓata mini rai. *(Ya yi tsaki)* Tsm! Wake yayin wannan yarinyar Lami yanzu. Hala! Dai baka ga yarinyar dana maye gurbinta da ita ba ne?

**Yautai:** A gaskiya Cinnaka baka da sabo. Amma in ban da haka Lami sakatariyace kuma da wuya ka sake samun kamarta.

**Cinnaka**: *(Ya yi tsaki)* Tsm! Kai kake ganin cewa Lami 'Yar goyo ce, amma mai ɗaki shi ya san inda yake masa yoyo. Kuma in banda kai Yautai ina zan ta zama da mace guda sai kace rai.

**Yautai**: Kai dai kawai ka ce ka gama cin moriyar ganga dan haka ka yada kaure.

**Cinnaka**: *(Ya gyaɗa kai alamar amincewa)* Ashe dai kana ganewa. Af! Baka tambaye ni sunan sabuwar sakatariyar tawa ba. Ai sunanta Rose.

**Yautai**: Don haka nake sonka mutumina, kamar ka san irinsu sun fi daɗin harkadon akwai su da bada haɗin kai sosai. *(Ɗantani ya kwankwasa ƙofar ofishin, ya shigo.)* A'a, Cinnaka ashe daman ka na ganin Ɗantani!

**Ɗantani**: Ai dama shi laifi tudu ne, amma in ban da haka ai kai zan cewa ashe rai kanga rai. *(Ya miƙa musu hannu suka gaisa)* Yautai ya ofishinku?

**Yautai**: *(ya amsa)* Ofis lafiya! Yaushe ka dawo daga kwas ɗin da naji an ce ka tafi yi a Jallah babbar Hausa. To, ina tamu tsarabar? Kar dai ka ce ka manta da mu a tsarabartaka.

**Ɗantani**: Wane ni! Sai kunzo karɓa a ofis ko gida za ku zo? *(Cikin fara'a)* Ai nakiyar dana riƙo bata ƙare ba tukun. Don haka ku kwantar da

hakalin ku tamkar tsumma a ruwa.

**Cinnaka:** *(Cikin wasa)* To, shi ke nan sai mun zo ofis inda gaske kake.

**Ɗantani:** Af! kar na manta, jiya fa an yi mini furomoshun! *(Yana murmushi)* kuma nan da wata uku zan je Landan wani kwas din sanin makamar aiki.

**Baki dayansu:** To, muna ta ya ka murna.

**Yautai:** Amma ya dace fa mu haɗa liyafa domin ta ya ka murna. Ka san irin wannan sai da ɗan holewa...

**Ɗantani:** *(Ya katse masa hanzari)* Haba! Yautai ai ba sai an yi Liyafa ba tun da tuni na sanya an yi saukar Ƙur'ani domin nuna godiyata ga Allah.

**Cinnaka:** Af! ai da ka yi maganar Liyafa sai ka tuna muni cewa Zainab jiya ta faɗa mini cewa larabar nan mai zuwa zata yi bikin tuna ranar haihuwarta *(Jinkiri)* Don haka naga ya dace na haɗa mata haɗɗaɗiyar Liyafa. Ko ya ka gani Yautai?

**Yautai:** Ai yin zai tabbatar mata da cewa kana ji da ita kamar kwai. *(Suka tafa)*

**Ɗantani:** Amma ni ina ganin yin hakan almubazzaranci ne kuma kun san yinsa ya saɓawa Musulunci.

**Cinnaka:** To, Ustaz, mun ji, Allah ya saka da Alheri Sarkin wa'azi. *(Ya miƙe bayan ya kalli agogonsa)* Don Allah ku yi haƙuri ina da mitin...

**Yautai:** Okee! To, sai mun haɗu ke nan. Amma fa kar ka bar ni na yi ta jiranka kamar jiya.

**Cinnaka:** Kar ka ji komai zan bullo da wuri Insha Allahu. *(Ya dubi Ɗantani)* Gida zaka isa ne ko ofishinka zaka koma?

**Ɗantani:** *(Sun nufi ƙofa)* Wallahi ofis zan koma! Cinnaka to yaushe zan dawo ke nan kan maganar Ɗanladin Malam Audun da muka yi da kai?

SERIAL/DOCUMENTATION UNIT
LIBRARY DEPT.
C.O.E. MINNA

**Cinnaka:** Okee! Batun taimakon da ka ce na yi masa ya koma ƙara karatu ko?

**Ɗantani:** Ƙwarai! Ka san yaron ya na da matukar ƙoƙari wajen karatu don haka tun da Allah ya sanya kai ne mai sanya hannu kan takardar amincewar komawarsa karatun naga bai dace a bar shi haka ba,domin nan da sati mai zuwa za'a rufe bada adimishun kamar yadda na samu labari.

**Yautai:** A gaskiya Ɗantani irinku ke shagwaɓa yaran nan. *(Ya yi tsaki)* Tsm! In ba shagwaɓa ba, yaron da yake aiki wane karatu kuma yake son ƙarawa. In dai ba so yake yi Cinnakan ya fita ya bar masa ofishinsa ba karatun da ya yi da,ai ya ishe shi.

**Cinnaka:** *(A fusace)* Haba! Ai linzami yafi ƙarfin bakin kaza. *(Ya dubi Ɗantani)* A gaskiya bana son yi maka alƙawarin da nasan cewa ba zan iya cika shi ba, don haka batun karatu nan na Ɗanladi a yanzu dai mu bar shi. *(Yautai ya gyaɗa kai na amincewa)*

**Ɗantani:** Haba! Kar mu yi haka da kai Cinnaka. Yaron nan fa kai ne mai ɗaga shi a wannan ofishin domin kai ne nasa. Kuma na gaya maka cewa saura mako guda kacal a rufe ɗaukar ɗaliban bana.

**Cinnaka:** Amma, Ɗantani kana bani mamaki *(Jinkiri)* Na faɗa maka cewa ina da mitin yanzu. Amma, tun da ka matsa shi ke nan zan bar shi ya tafi karatun amma babu albashi.

**Yautai:** *(Ya katse masa hanzari)* tsaya, tsaya don Allah Cinnaka... *(ya dubi Ɗantani)* Wai kai me yasa kake son nunawa yaran nan su Ɗanladi kai ne kawai mai son zumunci da taimakonsu.

**ƊANTANI:** Sam-sam ba haka bane. Amma dai Cinnaka don Allah kar mu yi haka da kai, ka taimaka.

**Cinnaka:** A gaskiya a hakan ma idan ya haɗa karatun ba zan sanya a yi masa furomoshun ba, don lokacin yi masa bai yi ba.

**Yautai:** Bari na raba muku wannan maganar. *(Jinkiri)* Hausawa dai na cewa, "Idan ruwan mutum bai isheshi alwala ba, sai ya yi

taimama".

Ɗantani: *(Cikin mamaki)* Yautai! Kana nufin yaron ya yi haƙuri ke nan da karatun kwata-kwata.

Cinnaka: Ƙwarai! Ai tuni abin da na ke nufi ke nan. *(cikin fushi)* Wallahi na rasa dalilin da duk lokacin da muka haɗu da kai Ɗantani, idan baka ci mana mutunci ba baka jin daɗi. Wato! Mu ba mu san dai-dai ba sai kai mai zumunci.

Ɗantani: *(Cikin sassanyar murya)* Kaga! Don Allah ku yi haƙuri *(Ya miƙa musu hannu, suka yi sallama)*. Ita dama gaskiya bata faɗuwa saboda ɗacinta *(Ya fita)*.

Yautai: *(Ya dubi Cinnaka)* Ban san ranar da Ɗantani zai san inda rayiwar yau tasa gaba ba. Shi ke nan sai mu kawo yara su san ashirinmu don muna son zumunci.

Cinnaka: *(Ya yi tsaki)* Tsm! Rabu da shi ya tsaya yana yaudarar kansa. Yau kowa ta kansa yake yi, kuma shi so ai so ne amma son kai yafi. Ko ba haka ba ne?

Yautai: Ƙwarai kuwa, maganar ka dutse mutumina!.

Cinnaka: Ai shi Ɗantani har yau bai san haka ba. Wai har da yin fushi ya wuce.

Yautai: Af! kai ka kula, in don tani ne umma ta gai da Aisha. *(cikin fushi)* Wai shi a ce yana da kirki. To, Audu Wazirin ɗanduna ai ya gama Wai shi a ce yana da kirki. To, Audu Wazirin ɗanduna ai ya gama magana cikin waƙarsa da yake cewa, "Duniya da wuyar zama, in ka yi kirki baka tsira ba..." Don haka in har ba mu tsira daga surutan jama'a ba, to shi ma bai tsira.

Cinnaka: Rabu da shi. In dai don jama'ar gari kar su zage shi ne yana da aiki a gabansa babba.

Yautai: Haka fa lokacin da ka fara neman Zainab ya dinga da mun ka cewar sai ka bar wa Bala yaron da har yanzu rarrafe yake yi bai miƙe ba.

**Cinnaka:** Lokacin nan babu irin ɓatanin da bai yi ba a gari, sai ka ce nayi mata dole don ta so ni, kwaɗayin abin hannuna yasa ta bar shi.

**Yautai:** In ban da wautarsa shima wace yarinya ce zata ga inda zata huta ta kai kanta in da zata wahala.

**Cinnaka:** *(Ya katse masa hanzari.)* Haba! Ai don haka lokacin na zubar mata da kuɗî kamar ban san darajarsu ba, saboda na saye imaninta. Kuma Alhamdulillahi domin haƙana ya cim-ma ruwa tun da yanzu na kusa fitar da kuɗina a jikinta.

**Yautai:** *(Suka tafa)* Ai na san baka wasa mutumina. Bare ma yarinyar da muka fahimci har yanzu zuciyarta na tare da Balan don rashin hankali.

**Cinnaka:** Ai sai tayi ta son sa, ni zare zaren ne nawa aikin, tun da bukatar maje Haji Sallah.

**Yautai:** Sosai kuwa! *(Jinkiri)* Kuma na san kana gama cin moriyar ganga zaka ya da kwauren. *(Suka tafa)* Sannan suka yi Sallama Yautai *(Ya tafi, shi kuma Cinnaka ya ƙarasa gun mintin ɗin da zasu yi a makare.)*

**FITOWA TA BIYU:** A KAN HANYA.

*Aminu na dawowa daga makaranta a ƙasa, sai ya haɗu da Abokinsa yaron Malam a kan hanya. Bari mu ji me suka tattaunawa. Ku biyo ni.*

**Aminu:** *(Shiga)* Wa nake hange kamar Yaron Malam *(Yana magana shi Kadai.)* Ai ko shine! Yaron Malam, Yaron Malam, *(Ya ɗaga murya)* Yaron Malam. *(Ya waigo)* Yaron Malam ina za ka ne haka naga kana ta sauri?

**Yaron malam:** *(Ya amsa)* A'a, Aminu kai ne cikin rana haka? Wallahi gida zan koma. Hala kai ma gidan ka nufa ne?

**Aminu:** Eee! Gida zani daga makaranta nake.

**Yaron malam:** Amma a gaskiya yau da gobe babu wuya a wurin Allah! *(Aminu ya gyada kai)* Ai jiya na ji su Malam Audu na cewa...

**Aminu:** *(Ya katse masa hanzari)* Suna cewa me?

**Yaron malam:** *(Ya amsa)* Wai badi zaka kammala karatunka na jami'a. *(Cikin damuwa)* Oh! Ina ma ni ne na samu wannan gatan da ka samu na shiga makarantar... *(Jinkiri)* Ai kaga ko babu komai in na kammala karatun, na kama wani aiki maimakon wannan dakon da nake zuwa kullum kasuwa ko tashar mota.

**Aminu:** *(Cikin mamaki da tausayawa)* Ai har yanzu baka makara ba. Ka san shi ilimi ba'a tsofa da yinsa. Amma, a gaskiya Yaron Malam ban san kana da sha'awar ilimin boko ba sai yau!

**Yaron malam:** Hmm! Kai dai bari faɗi Aminu! Ai ni wallahi ba kaunar barace-baracen nan da na sami kai na ciki nake yi ba!

**Aminu:** Wannan mukaddari ne, in ka kara haƙuri wataran sai labari. Kuma ai ilimin Muhammadiyyar da kake yi shi ne mafi mahimmanci a rayuwar mu ta musulmai.

**Yaron malam;** Maganarka gaskiya ce Aminu. *(Jinkiri)* Amma rayuwar yau ko musuluncinma na bukatar haɗa ilimin addini da na zamani kamar dai yadda kake yi din nan. Amma duk wannan laifin hukuma ne a nawa hangen.

**Aminu:** Kamar yaya ya zama laifin hukuma, Yaron Malam?

**Yaron malam:** Haba! Aminu ni nasan ka fahimce ni kai dai kawai kana son...

**Aminu:** *(Ya katse masa hanzari)* Kana nufin wai hukuma ta ɗauki nauyin ɗaukar ɗawainiyar kulawa da makarantunmu na Islamiyya da kuma na allo kamar yadda take yiwa na boko?

**Yaron malam:** Kwarai! Domin mu kan mu da mu ke yin karatun allon 'yan ƙasa ne! kuma hakkin hukuma ne ta kula da al'ummarta baki ɗaya, ba tare da nuna bambamci ba ko kuma son kai, ko maganar nan ba haka take ba ne?

**Aminu:** *(Ya buɗe baki, yana mamakin Yaron Malam)* A gaskiya yaron Malam maganarka haka take!

**Yaron malam**: To! In haka ne me ya sanya mu da muke yin makarantun allo da na Islamiyya hukumar bata biyan malamanmu albashi, da sama mana wurin kwana da kuma ajujuwan yin karatu? In da hukumar tana ɗaukar wannan haƙƙi nata babu yadda za'ayi malamanmu su dinga dogaro akan mu, bare har su dinga tura mu bara don neman abincin da za su ci da iyalansu, kafin mu sami wanda mu kan mu almajiransu zamu ci.

**Aminu**: *(Ya gyaɗa kai alamar amince)* A gaskiya hukuma ya da ce tayi wani abu akan wannan musamman ma yanzu da yake mulkin siyasa ake yi a ƙasar tamu. *(Sun iso inda zasu rabu)* To, Yaron Malam, ni zan isa gida. Sai an jima ke nan. *(Su kayi Sallama, ko wannensu ya kama hanyar zuwa gida.).*

**FITOWA TA UKU**: CIKIN MOTAR CINNAKA

*Hausawa dai na cewa, "sai hali ya yi ɗaya ake yin abota". Ga dai Cinnaka can da Yautai cikin mota sun nufi wurin da suke hutawa da 'yan matansu. Bari mu ji me suke kullawa:*

**Yautai**: *(Shiga)* Mutumin ban tambaye ka maganar ginin da kake ba? Kwana biyu ban ɓulla naga masu aikin ba, hala dai sun kammala shafa fantin da na bari a nayi?

**Cinnaka**: Haba! Ai tuni har an kammala zuba kujeru da sanya labulaye. Tarewa kawai ta rage nayi, in don ta Madam di nace, ai da tuni kaji mun tare mako biyu da suka wuce. Amma mako mai zuwa zamu tare!

**Yautai**: Ai da gaskiyarta, zaman lungu sai mara Naira!

**Cinnaka**: Kullum ita dai mu koma sabon gida shi ne zancenta. Ni kai na ina son hakan domin na gaji da zama cikin kunci. Sannan kuma duk da haƙurin da mutum yake yi da zama a cikin lungu, 'yan-uwa da makwaɓta ba su gani.

**Yautai**: Ai shi yasa tuni na bar namu gidan. Hala dai ba tare da Aminu zaka tare a sabon gidan naka ba ko?



SERIAL/DOCUMENTATION UNIT
LIBRARY DEPT.
C.O.E. MINNA

**[illegible]:** Aggasiya naso hakan, amma Madam ta nuna ranta bai so ba, don haka gidanmu zan bar shi. Kaga ni kai na na huta da bani-bani dak da dai ba bayarwar nake ba.

**[illegible]:** Au, tana da gaskiya! Yaushe zata bari ya biku, ya hana ku sakewa sosai. *(Suna isa otel din da suke holewarsu, sai suka fita daga mota; suka nufi ciki gunsu Rose sakatariyar Cinnaka a in da suke saba jiran su, suna holewa).*

*BAYAN SHEKARA UKU*

## SHIGA TA HUɗU

**FITOWA TA FARKO:** A KOFAR GIDANSU BALA.

*Bala da Yaron Malam suna zaune suna hira. Aminu na dawowa daga gidan Yakumbonsa Kande, har zai wuce sai ya gansu, don haka, sai ya tsaya don su gaisa. Bari muji me za su tattauna. Ku biyo ni.*

**Aminu:** *(Shiga)* Yaron Malam, salamu alaikum. *(Suka amsa)* Kai da Bala ne haka kuke hira!

**Bala:** *(Ya mika masa hannu)* Yaya kwana biyu unguwa ka fito ne haka?

**Aminu:** Wallahi gidan Yakumbona na fito To shi ne na ke son na ƙarasa gida ko na ɗan samu in kwanta na huta, don a gajiye nake. *(Jinkiri)* Kai! Allah ya sauwaƙewa talaka wahala!

**Bala:** Amin summa amin! *(Ya gyara zama)* In ce ko dai lafiya?

**Yaron malam:** Kai! Talaka a ƙasar nan na cin wuya sosai, ban da Allah da ya halicce shi babu mai son sa balle har ya sami mai tausayinsa.

**Aminu:** Ƙwarai! Maganarka babu tantama cikin ta. Sai dai abin takaicin shi ne, su kansu talakawan ba ƙaunar taimakawa junansu suke yi ba. *(Jinkiri)* In ban da haka yaya komai mutum yake son a yi masa, sai ya bada wani abu ko da mutuwa kuwa zai yi. Kai! Allah raba bawa da wahala. *(Suka amsa)* Ƙasar nan tamu anya abubuwa zasu yi dai-dai kuwa!

**Yaron malam:** To! Allah dai shiƙe masanin komai. Wataƙila lokacin ne bai yi ba na gyaruwar. Amma Insha Allah abubuwa zasu kyautata. *(Jinkiri)* Shugabanin ƙwarai muke buƙata masu kishin ƙasa da al'ummar su, komai zai gyaru!

**Bala:** Ai wato yaron Malam lalacewar ƙasar nan har mu kan mu waɗan da ake mulka halayenmu na buƙatar gyara.

**Aminu:** Babu shakka, yanzu kaga shekarata biyu har da watanni da kammala digiri na, ina ta zarga-zargar neman aiki, amma ya gagara. *(Ya dubi Yaron Malam)* Sannan kuma ba wai aikin ne babu ba kwata-kwata. *(Jinkiri)* A'a, aikin ne ya zama sai masu ido da kwalliɗa kuma 'yan matan da zasu iya sayar da mutuncinsu. *(Ya girgiza kai)* Kai! Allah ya sawaƙa mana wannan bala'i.

**Bala:** Amin summa amin.

**Yaron malam:** Al'amarin kan sai addu'a. Amma dai kam ba'a shuka gaskiya a ƙasar nan. In ban da haka Aminu da gama karatunka da yanzu aiki kam kana yinsa tun da wanɗanda basu da takardar shaidar yin makaranta kamar ka gasu nan suna aikin, don kawai suna da gata da ɗaurin gindi.

**Bala:** *(Ya gyaɗa kai)* Aiki kam yanzu, ya zama nawa kasani, domin an daina damuwa da ƙwarewar mutum sam-sam.

**Aminu:** Sannin hakan ya sanya nayi watsi da neman aiki kusan shekara guda da rabi yanzu. *(Jinkiri)* Na kama sama'ar wanki da guga. Amma rashin lafiyar da nayi watannin baya likita ya hana ni domin sanyi ya shigar mini jiki.

**Bala:** *(Cikin tausayawa)* Gashi kuma idan kasuwanci mutum yace zaya yi dole sai yana da jari mai ɗan kauri sosai.

**Yaron malam:** *(Ya dubi Aminu.)* Amma Yarinyar nan Merry da nake ganinku tare kuna zuwa makaranta, kafin ku gama, na ji ance Yayanka Cinnaka ne ya sama mata aikin da ta ke yi.

**Aminu:** Babu shakka! Shi ne domin da kanta ta faɗa mini cewar shi Yayan nawa ne ya sama mata.

**Bala**: *(Ya riƙe baki, yana mamaki)* To, in haka ne kaima ka same shi mana ka mika kukanka domin ya share maka hawaye.

**Aminu**: *(Ya yi murmushi, yana mamakin maganar Bala)* Kai dai Bala bar zancen kawai, domin shi yafi alheri. *(Jinkiri) Bala, kaima* dai sai kace ba ka san halin Yayana ba. *(Niyyar tafiya)* Allah dai ya taimake mu baki ɗaya mu da shi, ya kuma rufa mana asiri *(Suka amsa da Amin).*

**Bala**: Ai tun da ka ce haka shi ke nan. *(Ya mika musu hannu don su yi sallama.)* Amma dai su Yautai sun zama inuwar gigiya...

**Aminu**: Kai dai yi shiru domin mai ɗaki shi ya san in da yake yi masa yoyo!

**Yaron Malam**: Haka dai Hausawa suke cewa. *(Suka yi sallama dukkansu, kowanensu, ya nufi gida).*

**FITOWA TA BIYU**: A GIDAN SHAƘATAWAR CINNAKA.

*"Karshen alewa dai Kasa". In ji masu iya magana. Ga dai Zainab can da Cinnaka a gidansa na shaƙatawa. Bari mu ji wainar da suke toyawa. Ku biyomu:*

**Cinnaka**: *(Cikin faɗa)* A gaskiya haƙurin da nake yi da ke Zainab ya fa kai matuƙa, don haka daga yau, kar in sake ganin ƙafar ki ta tako mini gida ko ofishina domin shi haƙuri yana da iyaka. Ki na ji na ko?

**Zainab**: *(Cikin kuka)* Haba! Rabin raina. *(Ta sake fashewa da kuka).* Don Allah kayi haƙuri.

**Cinnaka**: Zance haƙuri bai taso ba! Matuƙar kina son kanki da mutunci, sai ki ji maganata kuma kiyi aiki da ita.

**Zainab**: Don Allah kayi haƙuri *(Ta matsa jikinsa).* In laifi nayi maka kafaɗa mini domin na guji maimaita shi. *(Hawaye na zuba daga idanunta).* Haba! Cinnaka ka tuna fa saboda matuƙar sonka daya mamaye mini zuciya, na rabu da tsohon masoyina.

**Cinnaka**: *(Ya ture ta daga jikinsa)* Abin da nake so dake shine ki kwashe 'yan komatsenki daga gidannan ki nufi in da dare ya yi miki.

**Zainab:** (*Cikin kuka*) Haba! Cinnaka ina kake son in tafi yanzu? Ka san dai da kunya in koma gidanmu domin saboda kai fa na gujewa iyayena dalilin dagewar da su ka yi cewa, "su Bala suke son na aura."

**Cinnaka:** (*Cikin fushi*) Kinga ni ban tanbayen ki wani tsohon labari ba. (*Ya nufi kofa.*) Maigadi, Maigadi kana ina ne? (*Maigadi ya shigo da sauri.*) Kafin na shiga wanka na fito, ka tabbatar Yarinyar nan ta dauke kayanta ta bace daga gidan nan sannan kuma kar ka sake barinta ta taka kafarta cikin gidan nan. (*Maigadi ya amsa.*) Ke kuma ga dubu daya nan kin shiga mota. (*Ya jefa mata.*) Ina fatan kin ji gargadin da na yi miki domin in kunne yaji to jiki ya tsira! (*ya shiga ban-daki, ya barta tana tattara kayanta cikin kuka*).

**FITOW TA UKU:** AMINU NA KABU-KABU.

*Aminu na dawowa daga kabu-kabu zuwa gida, sai Dantani ya tsayar da shi domin ya kai shi gida. Bari mu ji yadda za su kare. Ku biyo ni.*

**Dantani:** (*Shiga*) Dan-acaba! (*ya daga masa hannu, Aminu na tsayawa sai yaga ashe Dantani ne.*) Nawa zaka kai ni Unguwar sarkin Hausawa?

**Aminu:** Yaya Dantani kar dai in ce saukar ke nan?

**Dantani:** (*Ya dubi fuskar Aminu sosai*) Af! Aminu kai ne a she? Ai saukata ke nan! Yaya gida lafiya dai ko? Duk 'yan-uwa suna nan kalau ko?

**Aminu:** (*Bayan Dantani ya hau mashin*) Duk 'yan-uwa da mutan gida na lafiya! Amma fa yaya ka kwana biyu rabonka da kasar nan. (*Ya ja mashin suka nufi gida*).

**Dantani:** Ai shekarata hudu ke nan a kasar Rasha. Har yanzu baka kammala karatun ka ba ne?

**Aminu:** Ai shekarata uku ke nan da hada karatuna amma samun aiki yafi karfi na, domin ba irin kokarin da ban yi ba amma abin ya faskara.

**Dantani:** (*Sun isa gida*) Babu komai, in Allah ya so tun da na dawo.... (*Ya sauka daga mashin*) Bayan sati guda idan na koma aiki ka kawo

**Aminu:** To! Allah ya saka da Alheri. Na gode! *(Suka shiga gida, Aminu ya taya shi ɗaukar Jakarsa)* To, sai anjima. *(Fita).*

**FITOWATA HUƊU:** AƊAKIN BALA

*Hausawa dai na cewa "In farauta ta ki mutum ƙunkuru ma sai ya tsere masa." Ga dai Zainab can a ɗakin Bala tsahon saurayinta. Bari mu ji wainar da suke toyawa. Ku biyo ni.*

**Bala:** *(Shiga)* A'a, Zainab Ke ce yau a gidan nan. Hala dai ɓatan kai ki ka yi.

**Zainab:** Ai dama kai ne baka zama gida shi ya sanya in nazo ba na samunka.

**Bala:** *(Ya yi dariya)* To, na ji laifi na ne ke nan. In ce ko dai lafiya, tun da yau kin same ni?

**Zainab:** Lafiya ƙalau! Na dai zo ne na gaishe ka, *(Takwantar da murya)* sannan kuma na baka haƙuri... *(Jinkiri)* Bala, a gaskiya na san nayi maka laifi kuma ban kyauta maka ba. *(Ya yi shiru yana saurarenta)* Amma kuskure ne ya sanya na yi maka... *(Tana hawaye)* Don Allah Bala ka yi...

**Bala:** Haba! Zainab don Allah daina yin kuka, abin ai bai kai ga yin kuka ba. Rayiwa daman ta gaji haka don haka duk abin da kika yi mini na yafe miki don shi kansa Allah Gafurur Rahim ne! *(Ta ɗaga kai ta kalle shi)* Don haka ki share hawayenki, abin da ya riga ya faru babu yadda za muyi sai dai mu ki ya ye na gaba. *(Ta yi murmushi)* Amma sai dai akwai hanzari ba gudu ba.

**Zainab:** *(Gabanta ya faɗi)* Ina jinka! *(Ta yi masa fari da idonta)* Kai nake sauraro.

**Bala:** A gaskiya bai kamata na ɓoye miki zuciyata ba a yanzu. *(Ta kalle shi)* Ina mai farin cikin sanar miki cewa mako me zuwa za a daura mini aure. *(Ya dube ta)* Don haka a yanzu taimakon da zan iya yi miki shi ne naga kin ci gaba da makaratarki daga in da ki ka tsaya.

*(Tana ba shi haƙuri)* Zainab, a gaskiya batun aurenki da ni haƙuri za ki yi domin bakin alƙalami ya bushe.

**Zainab:** *(Ta durƙusa)* Don Allah Bala kar mu yi haka da kai *(Hawaye na zuba.)* Bala ka yi haƙuri don Allah.

**Bala:** *(Yana lallashinta)* Na san cewa ƙaddara cewa ta sanya maganar aurenmu da ke tahi ruwa, ba wai don ba kya so na ba. *(Ya miƙe)* Zan fita gun abokina Nuradeen don haka ki koma gida. *(Tana share hawayenta, ta fita daga ɗakin Bala, ta nufi gidansu tana cizon yatsan da na sani ƙeya ce)* Allah dai ya kyauta, shi ya sanya Hausawa ke cewa, "Kwaɗayi mabuɗin wahala." To, ni dai babu yadda zan yi domin ita ta jawowa kanta wannan kamun gafiyar Baiɗun da ta yi. Oh! Amma a gaskiya na tausaya mata. Wannan shi ne abin da Hausawa ke cewa, "Garin neman ƙiba an samo rama." *(Ya fita, yana tausayin cutar da Cinnaka ya yi mata).*

***BAYAN SHEKARA BIYAR***

**KASHI NA BIYAR.**

**FITOWA TA ƊAYA:** A OFISHIN AMINU.

*"Mai arziki ko a kwara ya sai da ruwa". In ji masu iya magana, kuma mai haƙuri ya kan dafa dutse.... Aminu kan haƙurinsa ya yi alfanu domin dutsen ya dahu kuma yanzu yana cikin shan romansa. Ga Yaron Malam can dai ya nufi ofishin Aminu. Bari mu ji mai za su tattauna. Ku biyo ni.*

**Yaron Malam:** *(Shiga)* Sallamu alaikum. *(Gaisuwa.)* Aminu yaya ofis! Komai dai yana tafiya yadda ya kamata ko?

**Aminu:** *(Ya amsa)* Alhamdulillahi. *(Jinkiri)* Yaya karatu? Har ka dawo daga laccar ke nan?

**Yaron Malam:** Wallahi yau ban sami zuwa ba, saboda ban ji ƙarfin jikina ba. *(Jinkiri)* Af! Ban tambaye ka ba, jiya ka kuwa kalli labaren ƙasa na ƙarfe tara na dare?

**Aminu:** *(Ya gyara zama)* Yaron malam akwai ka da jin labaru.

**Yaron Malam:** Ai mutuminka ko in ce yayanka Yautai gaskiya ta fara yin halinta.

**Aminu:** Kamar yaya fa?

**Yaron Malam:** Hmm! Ai don haka Hausawa ke cewa "Ramin ƙarya kurarre ne". Oh! Akwai azzalimai a ƙasar nan! In ba zalinci ba da kuma rashin tsoron Allah, a ce mutun guda kamar Yautai ya yi sama da faɗin miliyan sittin!

**Aminu:** Miliyan me?

**Yaron Malam:** *(Ya amsa)* Miliyan sittin! *(Ya riƙe baki, yana mamaki)* Oh! Rashin gaskiya ya zama ruwan dare a ƙasar nan! Allah dai ya sawaƙe. *(Aminu ya amsa)* Ai in kaga irin yadda 'yan sanda suka zubawa Yautai sarƙa....

**Aminu:** Subhanallahi! Ashe maganar ta yi ƙarfi.

**Yaron Malam:** *(Ya yi tsaki)* Tsm! Haka dai kake gani. Amma ba mamaki gobe kaga an wanke shi daga wannan tuhumar da za a yi masa.

**Aminu:** Maganar ka na da ƙamshin gaskiya. To, yanzu wani taimako kaga ya dace mu yi masa?

**Yaron Malam:** Haba! Aminu, taimako? Ai ba irin su Yautai ake tausayawa ba, bare har a taimakawa. *(Ya yi gyaran murya)* Ai tsuntsun da ya ja ruwa shi ruwa kan doka. Kuma tun da ya ɗebo ruwan dafa kansa namu sa ido!

**Aminu:** Wannan magana akwai ƙanshin gaskiya cikinta *(jinkiri)* Amma hannun ka ba ya rubewa.....

**Yaron Malam:** *(Ya katse masa hanzari)* Kar fa ka manta cewa, shi zalinci na da iyaka don haka mu sa ido kawai don ganin ko hukuma zata tatso dukiyar jama'ar da yaci. Taimaka masa ina ganin kamar ɗaurewa zalunci gindin zama ne!

inu: Eeh! Kai ma ka zo da hanzari mai ƙarfi.

ron Malam: Sam ba zata saɓu ba, wai bundiga a ruwa. Mun daina sa ido ana mai da dukiyar jama'a ta bilis. *(Ya miƙe)* Ni zan ƙarasa gida.

inu: To! Ga wannan ka shiga mota *(ya miƙa masa kuɗi)* Af! Aƙawarin kuɗin makarantar da na yi maka. *(Ya sake miƙa masa wasu kuɗin)* Don Allah ka yi haƙuri. *(Yaron Malam ya amsa, ya yi masa godiya ya fita zuwa gida).*

**OWA TA BIYU:** A MAJALISAR MATASA.

*Kowa ya sayi rariya ya san zata zubar da ruwa. Yantai dai tasa ta same shi domin kotu ayar da duk kadarorinsa domin ta biya gwamnati kuɗinta da ya handume. Bari mu ji yadda utai ya tsinci kansa cikin wannan hali. Ga dai Ɗanladi can da Aminu suna hira a majalisarsu. biyo ni.*

**inu:** *(Shiga)* Ɗanladi ashe haka wannan abu ya sami Yautai?

**nladi:** Wallahi! Abin dai babu daɗin ji.

**inu:** To, Allah dai ya sawaƙe. Na ji an ce wai tugun yaron nan ƙanin ƙabilar farkarsan nan ta unguwar dusten kura ne ya jefa shi cikin wannan halin da ya sami kan sa.

**nladi:** Ko shakka babu! *(Ya gyara zama)* Amma ai sai bango ya tsage kadangare ke samun wurin shiga.

**inu:** Ƙwarai! Kai amma Yaron ya ci amana domin ai shi mai rufawa Yautai asiri ne, musamman in ya duba irin taimakon da Yautai ya yi masa wajen tura shi karo karatu, ban da kuma kara masa mukami da ya dinga yi. Amma ji irin sakayyar da ya yi masa.

**nladi:** Ai na ji Musa makocina da ke aiki gun su Yautai ya ce Yaron ya yi hakan ne domin a dora shi kan kujerar shi Yautai din. *(Ya yi tari)*kuma hakansa ya cimma ruwa.

SERIAL/DOCUMENTATION UNIT
LIBRARY DEPT.
C.O.E. MINNA

**Aminu**: Ai don haka ake ce musu su rungumi nasu a jiki, amma sun ƙi ji. Ai ga irinta nan an gudu ba a tsira ba.. Ban da ma wauta mai zai sani na buɗewa bare cikina har ya san duk sirri na!

**Ɗanladi**: Ai a yau kuwa baren ake bayyanawa sirri a kuma ɓoye wa na jiki saboda albasa ba ta yi halin ruwa ba. Ni dai kan ban san in da mutan yau suka gado wannan hali ba domin iyayenmu ba su da aminai da suka wuce na jinkinsu..

**Aminu**: *(Ya hangi Bala tafe cikin sauri)* Bala lafiya dai ko?

**Bala**: *(Shiga)* To, lafiyar nan dai kam da sauƙi. Hala ba ku da labarin abin da ya sami Yaya Cinnaka da Madam ɗinsa?

**Aminu**: *(Hankalinsa a tashe)* Me ya sa me su?

**Bala**: *(Yana haki)* Ai 'Yan - fashi ne suka tare su.

**Aminu**: Subhanallahi *(Salati)* Ba su dai taba lafiyarsu ba ko? *(Ya yi zumbur, ya miƙe)* Yanzu suna ina?

**Bala**: Suna Asibiti (Jinkiri) To, sun dai yi wa Yaya Cinnaka raunuka. Ita kuwa Madam sun harbe ta.

**Ɗanladi**: Allahu Akbar! Allah ya jiƙanta, ya kuma kiyaye na gaba *(Suka nufi motar Aminu, suka shiga sannan suka nufi asibitin da aka kai su Cinnaka).* In ce ko dai ba su yi musu fashi ba ko?

**Aminu**: Anya kuwa. *(Yana tuƙi)*. Bala ka ce, "suna Babban asibiti ko?"

**Bala**: *(Ya amsa)* Can aka kai su! Ai 'Yan - fashin ba ƙaramin tarkonsu suka yi ba domin har motar Yaya Cinnaka suka yi awan gaba da ita ban da makuɗan kuɗi har dubu ɗari uku da hamsin. *(Suka nufi asibiti)* fita.

## BAYAN SHEKARA SHIDA.

**FITOWA TA UKU**: A KAMFANIN AMINU.

*Bayan shekaru Shida da fara aikin Aminu sai ya sami bashin Banki, ya kafa kamfani sufuri na motoci mai zamankansa. Ko da harka ta kankama sosai motocinsa suka bunƙasa, sai Aminu ya bar aikin gwamnati ya mai da kai sosai wajen kulawa da kamfaninsa. Ga dai Aminu can da Ɗantani a ofishin Aminu. Bari mu kasa kunne mu ji wainar da suke toyawa. Ku biyo ni.*

**Ɗantani**: *(Shiga)* Salamu Alaikum. *(Aminu ya miƙe daga kan kujerarsa da ya ga Ɗantani).*

**Aminu**: *(Ya amsa)* Wa Alaikumus salam! Barka da zuwa *(Ya nuna masa kujerar baƙi)* Bismillah, ga kujera nan. (Gaisuwa).

**Ɗantani**: *(Bayan ya zauna)* Yaya Aiki Aminu. *(Ya amsa)* Ah! Makasudin abin da ya kawo ni shi ne, *(Jinkiri)* Na yi maka godiyar abin farin cikin da na sami labari ka yi wa Yayanka Cinnaka *(Ya gyara zama)* Ina fatan za ka ci gaba da irin wannan halin.

**Aminu**: *(Ya danna karrawa, masinja ya shigo)* Na gode Yaya. *(Ya dubi masinja)* Don Allah Malam Baƙo maza ka samo wa Yayana lemo gun Mama Iyabo. *(Ya miƙa masa kuɗi, ya fita cikin sauri).*

**Ɗantani**: Haba! Ai da ka bar shi domin.....

**Aminu**: *(Ya katse masa hanzari)* Ai babu komai Yaya. *(Masinja ya dawo)* Yauwa! Malam Baƙo sannu da aiki, na gode! *(Ya a jiye lemon, ya fita)*. Yaya Bismillah. *(Ya miƙa masa lemon)* Kash! Sai kuma babu sanyi lemon.

**Ɗantani**: *(Ya amsa, ya fara sha)* Ai! Babu komai, ni kai na ban fiya son shan lemo mai sanyi ba.

**Aminu**: Bare ma gashi hukumar wutar lantarkin ma da ma ba barin wutar suke yi ba.

**Ɗantani:** Hmm! Ai harkar wutar lantarki sai lahaula domin abin kullum sake lalacewa yake sake yi.

**Aminu:** Ƙwarai! Allah dai ya kyauta kawai za mu ce. *(Ya gyara murya)* Yaya, na sami labarin cewa, "Kana son gina makarantar islamiyya irin ta zamani".

**Ɗantani:** Wallahi, tuni nake da wannan buri, *(Jinkiri)* rashin isassun kuɗi ne suka hana ni farawa.

**Aminu:** To, Yaya ai da zaka amince sai mu haɗa hannu tare mu gina domin ni kai na ina da irin wannan niyyya tuni.

**Ɗantani:** *(Cikin muma)* Amma a gaskiya na yi farin cikin sosai da wannan shawara taka domin na daɗe ina bin su Cinnaka don mu haɗa hannu domin ganin wannan buri na wa ya cika.

**Aminu:** Babu komai, Allah dai ya yi mana jagora *(Ya amsa)* Insha Allahu za mu gudu tare mu kuma tsira tare kan wannan buri.

**Ɗantani:** *(Niyyar tafiya)* Ni zan koma. Af! har zan manta ban yi maka godiyar Hajjin da na sami labarin an ce ka biya wa su Malam Audu da Malam Adamu da Malam Danjuma da kuma mahaifiyarta mu. Allah dai ya saka da Alheri ya kuma ƙara arziki.

**Aminu:** *(Ya amsa)* Amin summa amin! *(Rakiya)*

**Ɗantani:** Wannan alheri da kake yi yana da kyau sosai, *(Jinkiri)* Da man amfanin dukiyar ke nan mutum ya dinga taimakawa 'Yan-uwa da mabuƙata.*(Sun isa gun motar Ɗantani)* Sai an jima *(Ɗantani ya shiga motarsa, ya nufi gida)*. Fita.

**FITOWA TA HUƊU:** A CIKIN MOTAR CINNAKA.

*Wanda ya yi nisa ba ya jin kira. Cinnaka da Yautai duk da cewar sun rasa aikinsu a sakamakon rashin gaskiyar da suka shuka. Amma maimakon su yi hankali su san Allah ɗaya ne, sai suka ci gaba da sharholiyarsu. Da man Hausawa na cewa, "Haii zanen dutse". Bari mu ji me suke ƙullawa. Ku biyo ni...*

**Yautai**: (*Shiga*) Amma Yaronnan Aminu ba shi da hankali. (*Ya kalli Cinnaka*). Shi fa yanza gani yake don kana aiki a kamfaninsa har wani abin ba jin ta ya yi ko da yake don ya ga wuyansa, ya yi kauri ne, amma in ban da haka don motor da ya baka har ya isa ya dinga bin gari yana zaginka. (*Ya gyara murya*). Amma ba laifinsa ba ne domin wargi wuri shi ka samu kuma sai bango ya tsage....

**Cinnaka**: '(*Ya katse masa hanzari*) Kaga Yautai don Allah kar ka faɗa mini cewa, "Aminu yawo yake yi da ni a gari"(*Mamaki*) Amma a gaskiya Yautai tuni ya dace ka shai da mini wannan maganar, tun da nasan ko tusa akai yi a garinnan a idonka ake yi domin kai kunnen gari ne.

**Yautai**: (*Ya gyara zama*) Ka san ba na san ace ina neman haɗa ka da ɗan uwanka.

**Cinnaka**: (*Cikin fushi*) Amma lallai! Wannan Yaron Aminu sai na gwada masa cewar ni ba ɗan goyo ba ne. (Ya girgiza kai, yana huci.) Ni Cinnaka nake ban san na gida ba. (*Sun isa gun holewarsu Cinnaka ya sanya aka kawo musu giya*)

**Yautai**: (*Ya kurɓi giya*). Amma Yaron nan Aminu ya sake!

**Cinnaka**: Haba! Yautai mai kake ci na baka na zuba, ai dole ne a ramawa kura aniyarta. Har Aminu ya isa ya ci mana mutunci, ya kwana ƙalau.

**Yautai**: (*Ya fara buguwa*) Waa nee shiii!

**Cinnaka**: Ai tun da ya taɓa ni, (*Ransa a ɓace*) aika mini da shi lahira zan sa a yi. (*Dariya*).

**Yautai**: (*A buge*) Yauwa! Da man maganin shege ai sai ɗan kusun uwa. Kuma kaga in kayi haka shi ke nan sai ka zauna a kan dukiyarsa, duniya ta dawo mana sabuwa (*suka fashe da dariya*).

**Cinnaka**: *(Ya miƙe, yana tangaɗi)* Kai fa Yautai kamar tulu kake wajen shan ruwa. Ai sai ka tashi mu tafi gida in ba nan zaka kwana ba. *(Suka shiga mota a buge, suka nufi gida. Amma da yake Allah ba azzalimin bawansa ba ne sai suka yi hatsari a hanya, Yautai ya ce ga garinku nan take, shi kuma Cinnaka ya karya cinyoyinsa baki ɗayansu).*

**FITOWA TA BIYAR**: A KOFAR GIDAN MALAM ƊANJUMA

*To! Jama'a mun dai ga Karshen masu gina ramin mugunta. Don haka marigayi Dafta Mamman Shata ke cewa, "Mu gargaɗi mai gina ramin mugunta....." Da yake hassada ga mai rabo taki ce maimakon dukiyar Aminu ta yi baya, sai ta yi ta ƙara bunƙasa kamar ana sanya mata taki. Shi ko Cinnaka mai doki sai ya koma kuturi. Ga dai dattawan gari can suna hirar irin kirkin Aminu. Bari mu ji me suke cewa. Ku biyo ni.*

**Malam Ɗanjuma**: *(Shiga)* Alhamdulillahi! *(Ya dubi Malam Audu)* A gaskiya Malam Audu Yaron nan Aminu babu abin da zan ce masa illa Allah ya yi masa Albarka.

**Malam Audu**: *(Ya riƙe baki)* Ai ni har rasa abin da zan ce na ke yi duk lokacin da na ga ko ji irin abin arzikin da Yaron yake yi wa jama'a.

**Malam Adamu**: Ai sai mu yi wa Allah godiya da ya ba mu tsawon ran ganin.......

**Malam Audu**: *(Ya katse masa hanzari)* Ai Hakuri ta yi sa'ar haihuwar ɗa. *(Ya gyara murya)* Ai duk in da ka zauna hira, a garin nan ban da sawa Aminu albarka babu abin da zaka ji ana yi.

**Malam Adamu**: Kai dai dubi yadda ya rungumi ɗan-uwansa Cinnaka duk da irin rashin kyautawar da ya yi masa.

**Malam Ɗanjuma**: Mahaifi guda ai ba wasa ba ne!

**Malam Audu**: Na ji ma an ce ƙasar waje ya sanya aka fitar da Cinnaka domin nan babu kayan aiki sosai, a asibitin ƙasar waje sun fi kulawa da mara lafiya.

**Malam Adamu:** Ai ya kyata matuka gaya don in ban da shi da tuni an yanke kafar Cinnaka a nan.

**Malam Audu:** Tuni kuwa. Oh! Ina ma Allah ya nunawa Malam Sodangi irin makarantu da ɗan nan nasa Aminu yake ginawa *(jinkiri)*. Kai dai dubi yadda 'ya'yanmu da jikoki su ke ta girkuwa da ilimin Islamiyya da kuma shi kansa na bokon.

**Malam Adamu:** Haba! dubi dai yadda yaranmu da suka kammala karatun Jami'a suke samun aikin yi a kamfanonin da yake ta sake buɗewa.

**Malam Ɗanjuma:** Ai don haka Yaranmu da suke zaman kashe wando suna kuma shaye-shaye duk baka ganinsu yanzu saboda sun samu aiki a kanfanonuwan Aminun.

**Malam Adamu:** Ai da man rashin aikin ne ke haifar kaga samari suna samun kan su cikin irin waɗannan munanan halayen. *(Suka gyaɗa kai alama amincewa da maganarsa)* Yaushe rabonmu da jin wani na kukan an yi masa sata tun da ma su yi sun sami aikin yi!

**Malam Audu:** Ai wannan Yaro ba mu da abin da zamu yi masa sakayya da shi sai addu'a.

**Malam Ɗanjuma:** Ai kullum cikin yi masa ita muke!

**Malam Adamu:** Ƙwarai kuwa!

**Malam Audu:** *(Ya dubi Malam Adamu)* Wannan Yaron yadda yake son tallafawa al'ummarsa, in da da ne lokacin da muka yi siyasa irinta aƙida ba ta sai da 'yan ci ba ai da na tabbata yana cikin waɗan da jama'a zasu so yayi musu jagoranci.

**Malam Adamu:** Ƙwarai! Ai mai kishin cigaban al'ummarsa shi ne abin zaɓe ba 'yan-bani-na-iya ba, waɗan da ban da handume dukiyar jama'a zuwa aljihunsu babu abin da suka iya!

**Malam Ɗanjuma**: Ai wannan zamanin da muke ciki irinsu jama'a suke rubibin sawa ƙuri'arsu don tsabar da suke watsa masu kamar kaji.

**Malam Audu**: *(Cikin damuwa)* Ban san lokacin da jama'a zasu dawo daga rakiyar 'yan-kama-karya da kuma 'yan-hana-ruwa-gudun cikin 'yan siyasar mun ba. Mutane son kai dukiya ya mayar da su makafi.

**Malam Adamu**: Ai rashin idon ya san ya a yau jama'a ke faɗawa tarkon 'yan shigo-shigo ba zurfi kamar wasu marasa hankali da tunani.

**Malam Audu**: Ai son zuciya ba abin da bai haifarwa!

**Malam Ɗanjuma**: Allah dai ya kyauta. *(Suka amsa da Amin)* Ni zan shiga gida in ga halin da iyali ke ciki. *(Niyyartashi)* Wash! Jikin tsufa.

**Malam Adamu**: *(Ya dubi Malam Audu)* Malam Audu mu ma ai sai mu isa gidan ko?

**Malam Audu**: Eh! Amma inda da wani hanzari ba gudu ba.

**Malam Ɗanjuma**: Na me fa Malam Audu? To! Bismillah muna jinka.

**Malam Audu**: *(Ya gyara murya)* Tun da fatanmu al'amura su gyaru, me zai hana tun da zaɓe yana matsowa, mu bawa jama'ar gari shawara cewa su tsayar da Aminu ɗan takarar Zama.....

**Baki Ɗayansu**: *(Suka katse masa hanzari)* Wannan shawara taka Malam Audu ta yi kyau sosai, amma gaskiya kayi hangen nesa. *(Suka yi sallama, kowa ya nufi gidansa)*. Fita.

**ƘARSHE!!!**